RAMADAN MESSAGE BY PRESIDENT BUSH:

Ina son amfani da wannan dama domin isar da gaisuwa da fatan alheri ga dukkanin Musulmi anan Amurka da ko-ina a duniya, tare da taya su murnan shigowar wannan wata mai tsarki na Ramadan.

Watan Ramadan, wana ne mai tsarki ga dukkanin mabiya addinin Islama, domin a cikinsa ne Uban-giji ya saukar da al'qurani mai tsarki ga manzonsa, Mohammadu, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wannan wata na Ramadan, lokaci ne na ibada da tsarkake kai. Lokaci ne na gudanar da ayyukan sadaka da addu'a da duk wani al'amari na alheri. Lokaci ne da Musulmi a ko-ina suke a cikin duniya, suke kara jaddada dukufarsu kan rayuwa cikin yanayin tsarki, mutunci da tausayawa.

A dukkanin tsawon tarihinmu, mutane da suke bin addinai daban daban ne suka gina wannan kasa ta Amurka. Addinin Muslumci, addini ne na salama, kuma mutane da suke bin addinin Islama masu yawa sun bayar da gudumawarsu wajen gina wannan kasa da dukiya duka. A matsayinmu na Amurkawa, muna matukar girmama 'yancin addini kuma muna maraba da dukkanin mutane da addinansu. Muna bunkasa dimocradiya da falalarta, da yi mata kyakyawuyar fata ta hanyar habaka akidar 'yanci da fahimtar juna tsakanin jama'a duka.

Ni, tare da uwar-gina na, Laura, muna taya dukkanin Musulmi murnar shigar wannan wata mai tsarki na Ramadan.